# Na yi tafiya da Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- kuma ya kasance baya wuce raka'a biyu, haka ma Abubakar da Umar da Usman.

Daga Abdullahi Dan Umar -Allah ya yarda dasu- yace: "Na yi tafiya da Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- kuma ya kasance baya wuce raka'a biyu, haka ma Abubakar da Umar da Usman."
[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Abdullahi Dan Umar yana fada mana shi yayi tafiye-tafiye da Manzon Allah tsira da amincin Allah, hakanan yayi tafiye-tafiye da Abubakar da Umar da Usman Allah ya yarda dasu, kuma dukkaninsu sun kasance suna yin kasaru a sallolinsu masu raka'oi hurhudu,kuma basu yin sunnonin Rawatib a halin balaguro, ya ambaci Abubakar da Umar da Usman ne don ya nuna hukuncin baa shafe shi bayan wafatin Annabi ba yana nan tabbatace ne. Ya halarta a cika salla a halin balaguro, sai dai kasaru din ya fi; saboda fadinsa Madaukaki: {Ba laifa akanku da ku yi kasarun sallolin ku} fadin ba laifi da ayar tayi ya nuna cewa sauki ne aka bayar ba wai wajabci bane, saboda asali game da sha'anin salla shi ne a cika ta. abin da yafi ga matafiyi shi ne kar ya bar yin kasaru, saboda koyi da Annabi tsira da aminci su tabbata a gare shi, kuma don fita daga sabanin masu cewa yin kasaru tilas ne, kuma don kasancewar yin kasaru shi ne yafi gun malamai gaba daya.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee